Sarki ya sa aka tara masa manyan malamai guda casa'in na ƙasarsa.
أمر الأمير أن يُجمع له تسعون من كبار علماء بلده .

تسويرة ← Taswira :

تأتي بمعنى خريطة ، ويبدو أن هذه الكلمة ، نُقلت عن العامية المصرية

In kana son amsar wannan tambaya sai ka dauki taswirar Afrika.
إذا كنت تريد الاجابة عن هذا السؤال خذ خريطة أفريقيا .
Zana tswirar ƙasarku mu gani. ارسم خريطة بلدكم لنفهم .

Zanen taswira ba shi da wuya in ka koya.

رسم الخريطة ليس صعبا إذا تعلمت .

تعجب — Ta'ajibi أو Ta'ajjibi :

تأتي بمعنى عجيب

Waƙan nan mai ban ta'ajibi wadda muka ji jiya da dare.

هذا الشعر العجيب الذي سمعناه ليلة أمس .

Suka yi ta tu'ajjibi. تعجبوا كثيرا .

تعدّي — Ta'adda أو Ta'ada :

Ya yi ta'adda a kan kayan ajiya. تعدى على وديعة .

Mai ita yana da zaɓi , cikin kuɗin ko ƙimarta a ranar yin ta'adda.

صاحبها مخير في الثمن أو قيمتها يوم التعدي .

Ya tabbata tsohon nan ne , ya zo ya yi masa ta'adda.

تأكد أن هذا العجوز جاء وقام بالتعدي عليه .

Kafin arnan su ankara 'yan hari sun riga sun yi masa ta'ada.

قبل أن ينتبه الوثنيون ، بادر المغيرون بالتعدي عليه .

تعـذر — Taazzara :

Tasadar kaya ta'azzara a duniya. ارتفاع ثمن السلع في العالم جعل شراءها متعذراً .

Rashin lafiyar Ladi ta'azzara. مرض لادي تعذر شفاؤه .

Idan lamarin ya ta'azzara sai na haƙura. إذا تعذر الأمر لابد من الصبر .

تعـزية — Ta'aziyya :

Na tafi na yi wa lima ta'aziyyar babansa. ذهبت لتعزية الإمام في والده .

Ibrahimu shirya , mu je wajen ta'aziyya. ابراهيم استعد ، لنذهب للتعزية .

Da đana ya mutu Musa bai'zo mini ta'aziyya.

عندما مات ابني لم يأت موسى للتعزية .

تعاسة ← Ta'asa :

تأتي بمعنى الخسارة

Kar ka jawo mini ta'asa a cikin dukiyata. لا تسبب لي الخسارة في مالي .

Sa almubazzari a kan dukiya ta'asa ce a sarari. وضع المبذِّر على المال خسارة.

In ta'asa ta auku a dukiya ba magani sai hak̃uri.

إذا وقعت الخسارة على المال لا علاج إلا الصبر .

تعلق ← Ta'allak̃a :

Ya ta'allak̃a da đinkin. تعلق بالحياكة .

Ni ban ta'allak̃a da kowa sai Allah. لم أتعلق بأحد سوى الله .

Dukkan iyalina a kaina suka ta'allak̃a. كل أولادي تعلقوا ابي .

تَفَّ ← Tafa :

تأتي بمعنى بصق

Ya tofad da yawu. بصق اللعاب .

Na tofa masa addu'a a k̃afa. دعوت له وبصقت على قدمه .

Ta đebi ruwa , ta yi tofi , ta yafa mini sai na zama lafiyayye.

طلبت ماء ، وبصقت فيه ، ومسحت عليَّ ، فصرت معافاً .

: Tafsiri ← تفسير

Wane fanni ka ɗauka na ilmi ? fiƙhu ko tafsiri ?

أي فن من العلم أخذت ؟ فقه أم تفسير ؟ .

Babban mai tafsiri a birnin kano shi ne Nasiru Kabara.

دبر المفسرين في مدينة كنو هو ناصر كبرا .

Na fahimci tafsirin Jalalaini sosai. فهمت تفسير الجلاالين جيدا .

: Tafwili ← تفويض

Allah ya halatta auren tafwili. أحل الله زواج التفويض .

Auren tafwili shi ne auren da zasu daure shi ba tare da sun fadi sadaki ba. الزواج بالتفويض هو الزواج الذي يعقد دون ذكر الصداق .

: Taƙawa ← تقوى

Taƙawa a zuci take. التقوى في القلب .

Muhammadu Taƙiyin gaske ne. محمد تقي صادق .

Taƙiyanci ba aikin shashasha ba ne. التقوى ليست عمل البلهاء .

Ga yaƙi ga ilmi ga taƙiyanci. ها ــ المهارة ــ في الحرب والعلم والتقوى .

: Tallahi ← تالله

Wallahi tallahi ƙarya ne. والله تالله كذب .

Suka ce wallahi tallahi babu. قالوا والله تالله لا يوجد .

: Talbiyya ← تلبية

Ba zai daina yin talbiyya ba a ƙarshen ko wace salla.

لا يترك التلبية في آخر كل صلاة .

Zai ce gaba da yin talbiyya bayan gama ɗawafi.

يستمر في التلبية بعد الإنتهاء من الطواف .

: Tilawa ← تلاوة

Ba zai sujjadar AlƘur'ani cikin tilawa ba , sai in ya zamanto yana da alwalla. لا يسجد أثنا قراءة القرآن إلا إذا كان القاريء متوضأ .

'Yan makaranta sun Ƙari tilawa. تلاميذ المدرسة انتهوا من التلاوة .

Malam Garba ya iya tilawa المعلم جربا يستطيع التلاوة .

: Tama'imu ← تمائم

Ɗa ya gama ya shiga sulke da ɗamara da tama'imu.

عندما انتهي لبس اللبوس وحزام الذخيرة والتمائم .

Ba kowane malami ne ya san yadda ake yim tama'imu.

ليس كل عالم يعرف كيف تُصنع التمائم .

Mai tawak kali ba ruwansa da tama'imu.. المتوكل ــ على الله ــ لا يهتم بالتمائم

: Tamattu'i ← تمتع

Sifa tamattu'i kuwa ita ce ya yi niyyar yin umra wacce zata shiga kwanakin watannin hajji.

صفة التمتع هي أن ينوى العمرة في أيام الحج .

Kaɗaitawa ga hajji shi ya fi ga malikiyya daga yinta tare da tamattu'i ko kuma Ƙirani. الإفراد بالحج أفضل عند المالكية من التمتع والقِران .

Wanda ya yi tamattu'i kọ Ƙirani ba daga jama'ar Makka ba , to , hadaya ta wajaba gare shi. من تمتع أو قِرن من غير أهل مكة وَجَبَ الهدىُ عليه .

: Tuhuma ← تهمة

Ko shari'a ta halatta a yi tuhuma. حتى الشرعية أحلت أن يُتَّهم .

Ana tuhumarka ne game da Ƙagen cin hanci. أتهمت بتهمة أخذ الرشوة .

Ya ce wannan zato shi ya sa ya tuhumce shi.

قال هذا الظن هو السبب في أن يتهمه .

Wanda na taba na ji gabansa na faduwa shi zan tuhunta gobe.

من المسة وأشعر أن صدره يدق ، سأتهمه غدا .

Shaidar abokin husuma ko tuhuntacce ba ta halatta.

شهادة الخصم أو المتهم لا تجوز .

: Tuba ← توبة

Ya kamata ku tuba ku zama mutanen kirki.

يجب أن تتوبوا وتصبحوا رجالا صالحين .

Na tuba , na bi Allah , na bi ka. تبت واتبعت الله واتبعتك .

Ya riƙa tuba ga Allah mai tsarka tun gabanin ya nufi uƙuba a kansa.

يتوب إلى الله سبحانه قبل أن ينزل العقوبة به .

Bai halitta gare shi ba , ya jinkirta tuba. لا يحل له أن يؤخر التوبة .

: Tauhidi ← توحيد

Mai tauhidi sarkin ilmi. الموحد أمير العلم .

Tauhidi shi ne farkon rukuni a musulunci. التوحيد أول ركن في الإسلام .

Na fara karatun littafin tauhidi wajen Musa.

بدأت قراءة كتاب التوحيد عند موسى

Abin da ake so ya fara tabbata a zuciyar musulmu shi ne tauhidi.

المطلوب البدء بتأكيده في قلب المسلم هو التوحيد .

: Tawakkali ← توكل

Iliya ko yaushe mai tawakkali ne ga Allah. الياس دائما متوكل على الله .

Sai mu yi tawakkali ga Allah , wanda ke aikata kome yadda ya so.

يجب أن نتوكل على الله ، الذي يفعل كل ما يريد .

: Taimama ← تيمم

Maras lafiya yana yin taimama don yin sallar farilla ko nafila.

المريض يتيمم لأداء صلاة الفرض أو النافلة .

Ba'a yin sallar farillai biyu da taimama ɗaya.

لا تصلي فريضتان بتيمم واحد .

Ya yi taimama a farkon lokaci. تيمم في أول الوقت .

Taimama ana yinta a wuri ne mai tsarki kamar turɓaya.

التيمم يتم في مكان طاهر مثل التراب .

★★★

الثـاء

ثبت ← Tabbata :

Na tabbata ɗana ba ya sata. — تأكدت ــ أن ابني لا يسرق .

Ya tabbata babu jarumi kamarsa duk cikin taron.

تأكد ــ أنه ــ لا يوجد شجاع مثله في كل الجمع .

Iko ya tabbata ga Allah. — القدرة ثابتة لله .

Duniya ba gidan tabbata ba ce. — الدنيا ليست دار بقاء .

Allah yana tabbatad da waɗanda suka ba da gaskiya da faɗi tabbatacce.

يثبت الله الذين آمنوا بالقول الثابت .

Wannan abu tabbatacce ne. — هذا الأمر ثابت .

ثلث ← Sulusi :

Rabon gadon uwa daga ɗanta sulusi ne. — ميراث الأم من ابنها الثلث .

Ya shiga cikin sulusi biyu. — دخل في الثلث الثاني .

ثُلُثَيْ ← Talatain :

Can talatanin dare , sai ga sarki da waziri sun biyo ta nan.

بعد ثلثي الليل ، وإذا بالأمير والوزير يقصدان تلك الجهة .

Me ya sa ' aka sa ina ta dako a wannan talatainin dare ?

لماذا أمرت أن انتظر كثير خلال ثلثي الليل ؟

Da talatainin dare ya ga hadarin ruwa ya taso.

عند ثلثي الليل رأي عاصفة ممطرة تهب .

ثلاثين ← Talatin :

Aka yi lissafi aka tarar fam talatin. حُسِبَ فوجد ثلاثون جنيها .

A kan tara awaki wajen talatin ko arba'in.

يجمع عادة حوالي ثلاثين أو أربعين عنزة .

Ni yanzu a ƙalla na san kalma ta kusa talatin a cikin larabaci.

الآن اعرف على الأقل حزالي ثلاثين كلمة في العربية .

ثلاثاء ← Talata :

Zamu je bikin ranar talata. سنذهب إلى الفرح يوم الثلاثاء .

An sheƙa ruwan sama ranar talata. نزل المطر غزيرا يوم الثلاثاء .

Ba ni da aiki a makaranta ran talata. ليس لدي عمل بالمدرسة يوم الثلاثاء .

ثُمْن ← Tumuni :

Robon gadon sa shi ne tumuni. نصيبه في الميراث الثُّمن .

Tana da tumuni. لها الثُّمْن .

ثَمَنٌ ← Tamani :

Ya mutu ya bar tamanin fam hamsin. مات وترك ما ثمنه خمسون جنيها .

Fetur yanzu ba shi da tamani mai yawa. البترول الآن ليس غالي الثمن .

Dokina tamaninsa ba kaɗan ba ne. حصاني ثمنه ليس قليلاً .

ثمانين ← Tamanin :

Ya yi masa bulala tamanin don ƙazafi. جُلد ثمانين جلدة للقذف .

Wanda ya sha giya , a yi masa haddi bulala tamanin.

من شرب الخمر يقام عليه الحد ثمانين جلدة .

ثَنِيٌّ ← Saniyyi :

Saniyyi daga shanu shi ne wanda ya shiga shekara huɗu.

الثني من البقر هو ما دخل في السنة الرابعة .

★★★

الجيم

جائر ← Ja'iri أو Ja'iru :

Tanko duk inda ja'iri ya kai ya wuce nan.

حيثما وصل الجائر تنكو تجاوزة ، أي أنه فاق الجائر ظلماً .

Da ma sarkin wani ja'irin fasiƙi ne , kowa ya san shi a haka.

لقد كان أميرا جائرا فاسقا ، الجميع عرفة بذلك .

Allah ya kyasheka da sharrin ja'iru. حفظك الله من شر الجائر .

Ana nan dai har ya kai shekara goma sha biyar , amma ja'ircinsa sai gaba-gaba yake ci. وهكذا حتى بلغ الخامسة عشر ، ولكن جوره يزداد .

Ban ruwa ja'izi ne a bisa asali. سقاية الماء جائزة في الأصل .

Sanya tazali don magani ga maza ja'izi ne. وضع الكحل للتداوي للرجال جائز.

جائزة ← Ja'iza :

An bawa masu ƙoƙari ja'iza a makaranta. أُعْطِي المجتهدون جائزة في المدرسة .

Dokina ya cinye ja'izar sukuwar bana. حصاني نال جائزة السباق هذا العام .

Ba mai samun ja'iza sai mai ƙoƙari. لا نائل للجائزة إلا المجد .

جائفة ← Ja'ifa :

A kan bada sulusin diyya game da ja'ifa. يُدْفَع ثلث الدية للجائفة .

جبة ← Jabba أو Jibba :

Ba abin da ke kambama mutum irin ya sa wando mai zina da jabba.

لا شيء يشرف الإنسان كأن يرتدي سروالاً مزين وجبه .

Na saya jibba kyakkyawar gaske. إشتريت جبة جميلة جداً .

Jibbar malaman doguwa ce. جبة العلماء طويلة .

In ka je Magarib ka sayo mini jibba. إذا ذهبت — إلى — المغرب اشتر لي جبة.

: Jaddada ← جدد

Za'a jadada wannan hanyar banza. يُصْلح هذا الطرق عبثا .

Ya jaddada alwallarsa. جدد وضوءه .

Hukuma ta sa a jaddada masallacin kano. أمرت الحكومة أن تُجَّددَ مصلى كنو

: Jidali ← جدال

Mahajjaci ba'a yin jidali. الحاج لا يُجادل .

Jidali ba na mai aikin haji ba ne. الجدال ليس من شأن مؤدي فريضة الحج .

In jidali kake so , to , je ka , ka nemi abokin yi ' ni ba abokin yin ka ba ne.

إذا كنت تريد جدالا ، فاذهب ابحث عن محب للجدل ، أنا لست صاحبك في هذا الأمر .

: Jaza'atu ← جَذَعَةٌ

Jaza'atun ita ce taguwa 'yar rhekara biyar.

الجذعة هي الناقة ابنة خمس سنوات .

Idan yawansu ya kai sittin da daya za'a ba da jaza'atun.

إذا بلغ عددهم واحدا وستين يُعْطي جذعة .

: Jarraba ← جَرّب

Ya ba shi takarda da alƙalami ya jarraba shi. أعطاه ورقة وقلما ليجربة .

Yau ya kamata in jarraba ku. اليوم يجب أن أجرّبكم .

Ba mu zama ba sai cikin babbar gonar jarrabahuke-shuke.

لن ننزل إلا في الحقل الكبير للتجارب الزراعية .

Da aka yi jarrabawan nan , bai ci kome ba.

عندما أُجرى هذا الإختبار لم ينل شيئا .

An yi wa 'yan makaranta jarrabawa. أُجْرِي الإختبار لتلاميذ المدرسة .

Na ga wata jarababbiyar mata yau. رأيت امرأة شهوانية اليوم .

Turawa ba ƙananan jarrababbun mutane ba ne.

الأوربيون ليسوا أناسا قليلو التجربة .

: Jaraba ← جَرَبٌ

تأتي بمعنى البلاء

Taba ya zama jaraba gare shi. التبغ صار بلاءً بالنسبة له .

Allah ya kada mana jarabun nan. كشف الله عنا هذا البلاء .

Ya jaraba da ita. ابتُلِي بها ، أي أحبها حباً شديدا .

: Jarida ← جريدة

Karanta jarida yana da amfani. قراءة الجريدة مفيدة .

Babu jarida a ƙasar Hausa da ta fi «Gaskiya ta fi kwaɓo» shahara.

لا توجد جريدة في بلا الهوسا تفوق «جاسكيا تافي كوبو» شهرة .

: Girma ← جُرْمٌ

تأتي بمعنى كَبُرَ

In ta girma ba sa'a yi mata aure ba , sai ta balaga a gidan ubanta.

إذا كبرت لا تُزَوج حتى تبلغ في بيت أبيها .

Ga na girma ban san ko alifa ba. ها أنا قد كبرت ولم أعرف القراءة .

Ya ƙi zuwa domin girman kai. رفض الحضور تكبُّراً .

Saı da yawa zaka ga mutum , ka girmama shi , amma in ka bi cikin halinsa sai ka ga ba abin a girmama ba ne.

كثيرا ترى الرجل فتعظمه ، ولكن إذا تتبعت حاله لا ترى شيئا يُحْترم .

جزء ← Juzu'i :

Juzu'i shi ne yankin Ƙur'ani mai girma wanda ba cikakke ba.

الجزء هو جزء القرآن العظيم غير الكامل .

Kullum da safe ina karanta juzu'i guda. كل يوم أقرأ جزء واحدا .

Garba yana hardace juzu'i ɗaya a cikin mako guda.

أبوبكر يحفظ جزء واحدا في الأسبوع .

جزاف ← Juzufi :

Ba za'a yi canjin juzufi da juzufi ba. لا يُبَدَّل جزافٌ بجزافٍ .

جزماً ← Jazaman :

بمعنى قطعاً أو مؤكد

Wannan shi ne jazaman Ƙuri'ata ta masu gaskiya ne ba ta ɗan siyasa ba ne. اقتراعي هذا بالتأكيد اقتراع الصادقين وليس اقتراع السياسيين .

Jazaman ne zaman kafiri a wuta. دخول الكافر النار مؤكد .

Jazaman ne ka biya ni bashina. دفعك الدين لي مؤكد .

جزام ← Jizami :

Idan mace ta kamu ciwon jizami za'a mayar da ita gidan ubanta.

إذا أصيبت المرأة بالجزام ردت إلى بيت أبيها .

: Jaziya ← جزية

Ana karɓar jiziya ga mazaje ma'abuta amana da 'ya'ya balagaggu.
تُؤْخذ الجزيةُ من أهلِ الذمة والأوْلاد البالغين .
Sai su ba da jiziya. يجب أن يدفعوا الجزية .
Za'a nemesu ko kan musulunta ko kuwa su ba da jiziya.
يطلب منهم إما أن يسلموا ، وإما أن يدفعوا الجزية .
An karɓar jiziya ga mutanen da suka yarda zasu ba da ita bisa sharaɗin suna wurin da hukumcimmu.
تؤخذ الجزية من الناس الذين يقبلون دفعها تحت حكمنا .

: Giya ← جعة

تأتي بمعنى الخمر

A sawo giya a kawo tsakar fili , kowa ya yi ta sha ana annashawa.
أشتُريت الجعة وأحضرتها وسط الميدان ، وأخذ الكل يشرب حتى انتشي .
Wanda ya sha giya , a yi masa haddi bulala tamanin.
كل من شرب الخمر يُقام عليه الحد ثمانين جلدة .

: Jafa'i ← جفاء

Zai zama kamar abin jafa'i ne gare ni. سيصير مثل المكروه بالنسبة لي .
Kar ka yi wa ɗanka mummunan jafa'i.. لا تجفو على ابنك ــ جفاء ــ شديدا
Jafa'in mai jafa'i ya koma a kansa. جفوة الحقود ترتد عليه .

: Jalla ← جَلَّ

Jalla Sarki mai iyawa. جلَّ الملك القادر .

Jalla mai girma mai ɗaukaka. جلَّ العظيم المتعالي .

Jalla wa azza , ko yaushe yana tare da mai gaskiya.

جلَّ وعزَّ دائما مع الصادق .

: Jamratal Aƙabah — جمرة العقبة

Zai yi jifa a jamratal Aƙabah da tsakuwoyi gụda bakwai.

سيرم جمرة العقبة بسبع حصوات .

Ba zai tsaya a Jamratal Aƙabah ba sai ya wuce.

لن يقف عند جمرة العقبة ، يجب أن يمضى .

: Jima'i — جماع

A cikin barcinsa ya ga kamar yana yin jima'i. رأي في منامة كأنه يجامع .

Ba a yi jima'i tare da i'itikafi. لا يكون جماع مع الإعتكاف .

: Jummu'a — جمعة

Ya gina masa masallacin jummu'a wanda ba kamarsa.

بني له مصلى للجمعة لا مثيل لها .

Sallar jummu'a ba ta wuce su. صلاة الجمعة لا تفوتهم .

Jummu'a ba ta wajaba kan matafiya. الجمعة لا تجب على المسافر .

: Jama'a — جماعة

Jummu'a tana wajaba a cikin birni tare da jama'a.

الجمعة واجبة في المدينة مع الجماعة .

Yana wa'azi ga jama'a. يعظ في الناس .

Jama'a da yawa masu ƙaunarsa suka yi ta zuwa.

جماعة كبيرة ــ من ــ محبية حضروا .

A idon jama'a. على أعين الناس .

: Jam'i ← جَمْع

Yin jam'i a Arafat da Muzdalifa sunna ce wajiba.

جمع الصلاة في عرفات ومزدلفة سنة واجبة .

: Jami'a ← جامعة

Aminu ya koyi larabaci a Jami'ar Ummul Kura.

أمين يتعلم العربية في جامعة أم القرى .

Jami'a Ahmadu Bello babba ce. جامعة أحمدو بللو كبيرة .

: Jimla ← جملة

مجموعة كلمات مفيدة

Ka tambaye ni kan in rubuta maka jimla mataiƙaiciya.

سألتني أن اكتب لك جملة مختصرة .

A cikin wannan littafi akwai jimla da asalin furu'a da dangoginta abisa tafarkin Imamu Malik.

في هذا الكتاب توجد جمل من أصول الفقة وفنونه على مذهب الامام مالك .

: Jimla أو Jimilla ← جملة

بمعنى المجموع

A hada jimla bayi masu yawa a yanka musu fansa.

جُمِعَت جملةُ العبيد الكثيرين وأعتقوا .

An tara jimilla tasu. جمعت جملتهم .

: **Jamhuru** ← جمهور

An yi nini jamhuru. تجمهروا عليَّ .

Shi ne daga cikin 'yan iskan garin nan masu ƙulla mini sharri da jamhurun tsiya.

هو من الأولاد الفاسدين في هذه المدينة الذين يدبرون لي الشر وجمهور الفقراء .

: **Jana'iza** ← جنائز

تستعمل صيغة الجمع للدلالة على المفرد

Aka taru aka yi jana'izar , aka watse. تجمع الناس ، وأقيمت الجنازة وانصرفوا .
Na yi shiri mu tafi wurin jana'iza. لنستعد ولنذهب إلى الجنازة .
Na ga taron mutane bilahaddin fari fat ana jana'iza.
رأيت جمعا كثيرا من الناس بيض الثياب يشيعون الجنازة .
Shigewa gaban jana'iza wajen raka shi ya fi. السير أمام الجنازة أفضل .

: **Janaba** ← جنابة

Wanka na wajaba da sababin abu uku , janaba da haila da jinin biƙi.
الغسل وجب بسبب ثلاثة أشياء ، الجنابة والحيض والنفاس .

Bai halatta ba ga mai janaba ya shiga masallaci.
لا يحل لذي جنابة أن يدخل المسجد .
Janaba shi ne fitan maniyya da jin daɗi na al'ada a cikin barci...
الجنابة هي خروج المني مع اللذة المعتاده في النوم ... .

: **Jinsi** ← جنس

بمعنى صِنْف

Ana tara jinsin dabino shi ma a yi masa zakka.

جُمع أصناف التمر ودفع له الزكاة .

Ana iya tara jinsin auduga a yi mata zakka.

يمكن جمع أصناف القطن ودفع الزكاة عنها .

: **Aljanna** ← جنَّة

Ya shigad da shi aljanna tasa da immaninsa. . أدخله ـــ الله ـــ جنته بإيمانه

Hakika , aljanna gaskiya ne. . إنَّ الجنة حقٌّ

Allah ya halicci aljanna ya tanade ta gidan dawwama ne ga waliyyansa.

الله خلق الجنة وأعدها دار خلود لأوليائه .

: **Aljani** أو **Aljannu** ← جِنٌّ

Ya nufi gidan sarkin bokaye ya ce ya taimake shi da maganin ' aljannu sun taba shi.

قصد منزل كبير المشعوذين وقال أن يساعده بدواء الجن لأنهم مسوه .

Tana tasammani uwata mutum ce , ba ta san aljanna be ce.

كانت تظن أمي إنسانة ، ولم تعرف أنها جنية.

Nan da nan ya koma siffar aljannu. . في الحال عادت إلى صفة الجن

Ko aljani ya yi kokari ya isa dutsen nan sai wani ikon Allah.

حتى لو حاول الجن أن يصل إلى هذا الجبل ـــ لا يستطيع إلا بقدرة الله .

: **Jinaya** ← جناية

Hukucin jinaya a musulunci ba abu ne mai sauƙi ba.

حكم الجناية في الاسلام ليس أمرا سهلاً .

Na binciki kaifiyyar jinaya a musulunci. بحثت كيفية الجناية في الاسلام .

: **Jiha** ← جهة

Na nufo wajen jihar Sudan. قصدت جهة السودان .

Suka tasam ma jihar da ayarin suka bi. توجهوا إلى الجهة التي اتبعتها القافلة .

Muka yi ta tafiya , ni ban san jihar da muke nufa ba.

سرنا كثيرا ، وأنا لا أعرف الجهة التي نقصدها .

: **Jihadi** ← جهاد

Jihadi farilla ne da wani ke ɗauke wa wani.

الجهاد فريضة يحمله بعض الناس عن بعض .

Mun shirya, mu je mu fara jihadi da su.. استعدينا لنذهب ونبدأ الجهاد معهم

Shaihu ya ci gaba da sha'anin jihadi. استمرار الشيخ في الاستعداد للجهاد .

: **Jahili** ← جاهل

Na zaɓi jahili na ɗaukaka shi har da yi masa sarkin fada.

دثرت جاهلا ورفعته حتى جعلته رئيس القصر .

Nomau ya tafi ya bar jahilin nan yana ta jira.

ذهب نُومَوْ وترك هذا الجاهل يطيل الأنتظار .

Ya Allah ka kyashe mu da aikin jahilai. يالله قنا عمل الجاهلين .

Babu abin da ya fi jahilci duhu. لاشي يفوق الجهل ظلاما .

Ya kau da ni cikin wannan jahilci. أخرجني من هذا الجهل .

Ilmin da ba zai yi amfani ba , kuma jahilcin da ba zai yi cuta.

علم لا ينفع ، وجهالة لا تضر .

Allah ya tafiyar muku da girman kan nan na jahiliyya.

أذهب الله عنكم كبر الجاهلية .

Gaya mana labari mu ji guda , na ɓarayin lokacin jahiliyya.

قل لنا قصة واحدة من ـــ قصص ـــ اللصوص في عصر الجاهلية لنسمع .

: Jahannama ← جهنَّم

Wasu ayyukansu su jefa su a cikin wutar Jahannama.

بعضهم تلقيهم أعمالهم في نار جهنم .

Ka tsare shi daga azabar ƙabari da kuma azabar Jahannama.

نَجِّهِ من عذاب القبر وعذاب جهنَّم .

: Jawabi ← جواب

تأتي بمعنى كلام

Sarki ya yi shakkar wannan jawabi. الأمير شك في هذا الكلام .

Mai kuɗin nan ya mai da jawabi duka. صاحب المال كرر الكلام كله .

Da sarki ya ji jawabin matan nan sai ya fahimta.

عندما سمع الأمير كلام هذه المرأة فهم .

: Jaura ← جولة

Na gaji da jaura na ga nan zuwa can. تعبت من التجول من هنا إلى هناك .

Takalmina ya koke sabo da yawan jaura. حذائي اشتكي من كثرة التجوال .

Musa ya dawo daga jaurace - jauraci. عاد موسى من جولاته .

: **Jauhari** ← جوهر

Muna da dukiya zinari da azurfa da jauhari iri-iri.

لدينا الثروة ــ من ــ ذهب وفضة وجوهر أنواع .

A ƙarƙashen kogi ake samun jauhari. في قاع البحر يوجد الجوهر .

Kayan adon mata wanda ake yi su da jauhari tsada ne da su.

حلى المرأة التي تصنع من الجوهر غالية .

: **Aljihu** ← جَيْب

Ya sa hannu aljihu ya kawo sisi. وضع يده في الجيب وأخرج مليما .

Ta ba shi , ya sa aljihu , ya shiga gida. أعطته فوضعه في جيبه ودخل المنزل .

Ya naɗe takarda ya sa aljihu. لفّ ورقة ووضعها في جيبة .

★★★

الحاء

: Hubusi ← حُبُس

Hubusi shi ne sanya amfanin wani abu sadaka ga hanyar alheri.

الحبس هو جعل عائد شيء صدقة في سبيل الخير .

Akwai wani sharadi a asalin hubusi. يوجد شرط في أصل الحبس .

Ba a sayad da hubusi ko da ya rushe. لا يُباع الحبس ولو خرِب .

Kyauta ko sadaka ko hubusi ba su cika sai tare da shiga hannu.

الهبة أو الصدقة أو الحبس لا تتم إلا بالحيازة .

Ya hubusce gida. حَبَس داراً .

: Hatta ← حتى

An sace masa kaya , hatta takalmi ba a bar masa ba.

سُرِق منه المتاع ، حتى الحذاء لم يترك له .

Hatta man fitila sai da uwargidanka ta aiko mata da shi jiya.

حتى زيت المصباح ربة بيتك بعثت به إليها أمس .

Ba wanda ya san ubansa , hatta ma yara , abokan wasansa.

لا أحد يعرف أباه ، حتى الأولاد كذلك ، رفاق لَعِبِه .

: Hajji ← حَجٌّ

Yana bata hajjinsa. يفسد حَجَّه .

Na raka sarkin arewa hajji. رافقت أمير الشمال في الحج .

: **Alhaji** ← حـاج

Ba a ga kowa ba sai wani alhaji. لم ير أحدا سـوي حاج .

Aka sa mini sunan alhaji Imam don ranar hajji aka haife ni.

سميت الحاج إمام لأني ولدت في يوم الحج .

Suka gamu da wani ayari na alhazai zasu Makkah.

قابلوا قافلة للحجاج ذاهبة إلى مكة .

Sun saye da tufafi irin na larabawa sun yi shigar alhazai.

اشتروا ثياب مثل ثياب العرب ودخلوا كالحجاج .

: **Hujja** ← حُجَّةٌ

Allah ya aiki ma'aikansa zuwa gare su , domin tsayad da hujja bisa gare su. أرسل الله رسله إليهم لإقامة الحجة عليهم .

Hauka ja zuwa kasuwa ba hajja ba hujja.

جنون ، الذهاب إلى السوق بلا سلعة سبب .

Wannan hujja da ka kafa bidi'a ce. هذه الحجة التي أقمتها بدعة .

Ba wata hujja ba kuwa wani dalii. لا حجة ولا دليل .

Ina hujjar wannan ? ما سبب هذا ؟

: **Hajja** ← حاجَةٌ

تأتي بمعنى سلعة

Ya karɓi hajjarsa idan har za a iya gane ta ainihinta.

أخذ سلعته إذا أمكن معرفتها بعينها .

Kafin zuwan turawa , ba mu da hanyar ta daukar hajja daga wannan gari zuwa wannan , sai jakana,

قبل مجيء الأوربيين ، لم يكن لدينا طريق لأخذ السلعة من هذه المدينة إلى تلك إلا الحمير .

Hauka , ja zuwa kasuwa ba hajja ba hujja.

جنون ، الذهاب إلى السوق بلا سلعة ولا سبب .

Motocin nan suke kai wa Ƙasashen hajjar turai.

هذه السيارات تنقل إلى البلاد سلعة الأوربيين .

Ya labta wa jakuna ko takarkarai hajjoji da goro.

حَمَّل الحمير والثيران السلع وثمار الكولا .

Yana sayad da hajjoji. ربيع السلع .

: Hajarar Aswad ← حجر أسود

Ya sumbanci Hajarar Aswad da bakinsa. قَبَّل الحجر الأسود بفمه .

Zai sumbanci Hajarar Aswad tare da yin kabbara.

يُقَبِّل الحجر الأسود مع التكبير .

Ya sake sumbantar Hajarar Aswad in ya sami iko.

يكرر تقبيل الحجر الأسود إذا وجد القدرة .

: Haddi ← حد

Yana wajabta haddi. يستوجب الحد .

Ba yin haddi a kan wanda bai isa mafarki ba.

لا يُقام الحد على من لم يبلغ الحُلُم .

Ba a yin daddi ga mai yin wa yaro Ƙazafi.

لا يقام الحد على قاذف الصبي .

Ya wajaba gare shi ya kiyaye haddodin Allah.

وجب عليه أن يحافظ على حدود الله .

Akwai bambanci a wajen ma'anonin haddodi.

يوجد خلاف حول معاني الحدود .

حَدَث — **Hadas** :

Wanka na wajaba daga hadasi. وجب الغسل من الحدث .

Tsarki ya kasu kashi biyu ne , tsarkin hadasi da tsarkin dauɗa.

الطهارة تنقسم قسمين ، طهارة حدث وطهارة خبث .

حَدَّث — **Haddace** أو **Hardace** :

تأتي بمعنى حفظ أو كتب

Abin da nake so , sai ko haddace abin da na koya muku.

ما أريده ، أن تحفظوا ما علمتكم .

Bayan kwana uku kowa ya hardace. بعد ثلاثة أيام الكل حفظ .

Ka zauna nan , ka hardace wannan labari sa'an nan ka tashi.

إجلس هنا احفظ هذه القصة ثم قم .

Ya yi kyan mu shawarci malamai , su yi ƙoƙari su hadasa labaru da Hausa.

الأحسن أن نتشاور مع الأساتذة ، ليحاولوا كتابة قصص الهوسا .

(...)

حديث — **Hadisi** :

Ya zo cikin hadisi cewa a yi umurni ga yara da yin salla.

جاء في الحديث أن يؤمر الأولاد بالصلاة .

Akwai wani hadisi wai wata rana wani ya aza wa jakinsa kaya , ya bi shi yana tafe yana duka.....

يوجد حديث أن يوما وضع شخص على حمارة المتاع وتبعه يسير ويضرب... .

Kowa garin ya ji na kwana hadisi.

كل من في المدينة سمع ــ أنني ــ قضيت الليل أحدث .

حـاذق ← Haziƙi :

Ko ina haziƙi ya shiga ya sami masaya. حيثما ذهب الحاذق يجد الأحباب .

Hazaƙa da daɗi take a rayuwa. الحذاقة مفيدة في الحياة .

حـرب ← Harba :

تستعمل بمعنى الصيد ، أو اطلاق السهم أو اللدغ

Wani maharbi ya harbe ta. صياد اصطادها .

Da ta ji zafi sai ta harbe shi. عندما شعرت بالحرارة لدغته .

Ya ja baka zai harbe shi. شـد القوس ليطلق عليه السهم .

Sarkin Gobir ya daga bindigar da ke gare shi zai harbi shaihun , bindigar ta fashe.

أمير جوبير رفع البندقية التي لدية ، سيطلق النار على الشيخ فانفجرت البندقية .

حرير ← Alharini :

Wanda ya yi salla da alharini ya yi saɓo amma sallarsa lafiya lau take.

من صلى بالحرير عصى الله ، ولكن صلاته صحيحة .

A hana maza sanya tufafin alharini. نُهِيَ الرجال عن لبس الحرير .

Kayan da ake kawowa daga arewa ita ce alharini.

المتاع الذي يجلب من الشمال هو الحرير .

حرف ← Harafi :

Ya yi tafi cikin tufansa ba tare da fidda harafi ba.

نفث في ثوبة دون أن يخرج حرفاً .

Wanda ya yi nishi a cikin sallarsa babu kome a-kansa sai fa in ya furci da haruffa.

من تنهد في صلاته لا شيء عليه إلا إذا نطق بحروف .

Me waɗannan haruffan masu bin juna suke nunawa.

ماذا تعني هذه الحروف التالية لبعضها .

: Hirfa ← حرفة

Dole ne , mutun ya sami hirfa da ya yi.

لا بد أن يجد الإنسان الحرفة التي يقوم بها .

Da mutum ya roƙo gwamma ya nemi ko wace hirfa ya yi.

أن يبحث الإنسان عن حرفة يعملها خير له من السؤال .

Dogara a kan hirfa ya fi dogara a kan gado.

الاعتماد على الحرفة أفضل من الإعتماد على الميراث .

: Harka ← حركة

تأتي بمعنى حركة أو عمل

Ya harɓe , sai harka yake yi , wai ya zama sarki.

تربع وأخذ يتحرك كأنه صار أميرا .

Ba ya harka da hannuna. لايتحرك بيده .

Ina da harka cikin gida. توجد حركة في المنزل .

Da isarsa garin da zai tambayi gidan wani mai harka ya je ya yi barantaka.

عندما وصل المدينة سأل عن منزل رجل أعمال ليخدم لديه .

In Allah ya yarda zan ci gaba da harkokina gobe.

إن شاء الله سأستمر في أعمالي غدا .

Allah shi ne mai ƙaddara harkokinsu da ajalinsu

الله هو المقدر حركاتهم وآجالهم .

: **Hurumi** ← حُرُم

الأماكن التي تقام فيها المقابر

Ya tashi ya yi ta yawo har ya kai hurumin mutanen gari.

قام وتجول كثيرا حتى وصل مدافن أهل البلد .

Aka kai hurumin da aka haƙa masa kabari , aka ɗauke shi aka jefa ciki. وصلوا المدافن التي حُفِر له قبرٌ فيها ، وأُخِذ وأُلْقِي فيه .

Ya tafi hurumi , ya duba wani sabon kabari ya tone ya ɗauko gawar ya kawo gida,

ذهب إلى المدافن ، بحث عن قبر جديد ، حضر وأخذ الجثة وحملها إلى المنزل .

: **Haramta** ← حَرَّم

Duk waɗannan abubuw sun haramta ga mutum.

كل هذه الأشياء حُرِّمت على الإنسان .

Ya dubi abin da aka haramta masa dubawa.

نظر — إلى — ما حُرِّم عليه رؤيته .

Ta haramta ga iyayensa kamar haramtawar aure.

تحرم على آبائه كتحريم النكاح .

Yin sulhu ya halatta sai dai sulhun wanda ya kawo haramci.

الصلح جائز إلا الصلح الذي جلب حراماً .

Ya wajaba gare shi ya kiyaye ganinsa daga ganin haramun.

وجب عليه أن يحفظ بصرة من رؤية الحرام .

Daga farillam salla niyyar salla mu'ayyana da kabbarar harama.

من فرائض الصلاة نية الصلاة المعينة وتكبيرة الإحرام .

Daga mustahabban salla ɗaukaka hannuwa gun harama.

من مستحبات الصلاة رفع اليدين عند الإحرام .

Ya wajaba a gare shi ya dauki harami daga Miƙatin ƙasarsa.

وجب عليه أن يُحْرِم من ميقات بلده .

An umurci mai yin hajji ya yi wanka yayin ɗaukar harami.

أُمِرَ مؤدي الحج أن يغتسل عند الإحرام .

Mace zata sanya huffi da tufafi a cikin haraminta.

المرأة تلبس الخف والثياب في إحرامها .

حِزْب ← Izifi أو Hizifi :

Alƙu'ani 'izifi sittin ne. القرآن ستون حزباً .

Na sayi juzu'in ƙur'ani mai hizifi goma.

أشتريت جزء من القرآن من عشرة أحزاب .

حزن ← Huzunu :

Allah ya kore mana huzunu. اللهم أبعد عنا الحزن .

Ba abin da ya fi kome huzunu a duniya kamar samun lalataccen da.

لا شيء في الدنيا اكثر حزنا من أن يرزق الانسان طفلا فاسدا .

Mumminai ba ruwansu da huzunu ranar ƙiyama.

لا يعرف المؤمنون الحزن يوم القيامة .

حساب ← Lissafi ≥ Hisabi :

Ya manta da lissafin ramuwa da ke kansa. نسي عدد القضاء الذي عليه .

Aka yi lissafi aka tarar talatin da biyu ne.

حسب فوجد ـ أنه ـ اثنين وثلاثين .

Ba mu sa su cikin lissafi. لم تضعهم في الحساب .

Har yau shi ne ake lissafinsa cikin masu arzikin ƙasan nan.

حتى اليوم يُحسب في أثرياء هذه المدينة .

Za'a yi masa hisabi mai sauƙi. سيُحاسب حساباً يسيرا .

Domin bijirad da al'umma da hisabinta da azabarta da ladanta.

لعرض الأمة وحسابها وعقابها وثوابها .

حسد ← Hassada أو Hasada :

Da sarki ya ji haka , sai ya yi tsammani hassada ce.

عندما سمع الأمير ذلك ظن حسداً .

Da azziki da hasada tare suke kwana. الرزق والحسد يتلازمان .

Allah ka kore mana huzunu da hassadar. اللهم أبعد عنا الحزن والحسد .

حشفة ← Hashafa :

Hashafa ita ce kan azzakari. الحشفة رأس الذكر .

Janaba shi ne fakuwan hashafa a cikin farji.

الجنابة هي غياب الحشفة في الفرج .

حصل ← Hasala :

تأتي بمعنى غضب أو فعل

Wannan sabon shugaban bai hasala hasala kome ba har yanzu.

هذا الرئيس الجديد ما فعل شيئا حتى الآن .

Malam Musa yana da saurin hasala. الأستاذ موسى سريع الغضب .

Idan na samu kudi zaka ga abin da zan hasala,

إذا وجدت المال سترى ماذا سأفعل .

حاصل ← Hasili :

تأتي بمعنى الأفضل

Hasili ma dai tafi abinki kada ki ƙara wahalad da ranki a banza.

الأفضل أن تذهبي لشأنك ولا تتعبى نفسك أكثر بدون فائدة .

Hasili ma dai sai ya auri 'yar sarkin garin nan.

الأفضل أن يتزوج ابنة أمير هذه المدينة .

حضر ← Hallara أو Halarta :

Sarki ya ga duk an hallara tun da sassafe.

رأي الأمير أن الجميع حضروا منذ الصباح الباكر .

Kowa da kowa ya hallara. الجميع حضروا .

Ya halarci jana'izarsa. حضر جنازته .

Ya tara yara yana zana musu yaƙoƙin da ya halarta duka.

جمع الأولاد وأخذ يقص لهم الحروب التي حضرها كلها .

Ba wata masifa da take samunka a cikin halartar wadannan wurare.

لا توجد مصيبة تصيبك في هذه الأماكن .

Ya halartad da zuciyarsa ga Allah kaɗai. حضَّر قلبه مع الله فقط .

حق ← Hakki أو Alhaki :

تأتي بمعنى الحق أو الذنب

Kowa ya sami abin da ya fi hakkinsa. كُلٌّ نال مافاق حقه .

Sarki bai cika maganarsa ba , tun da ya hana ni hakkina da na cancanta.

الأمير لم يف بكلامه ، طالما منعني حقي الذي استحقه .

A karɓi hakkokin mutane , na daga dukiya ko jini.

أُخِذَ بحقوق الناس من مال أو دم .

Kana so ka gudu , sai alhakina ya kama ka.

أردت أن تهرب ولكن حقي أمسكك .

Zan tafi neman abin da zan rage alhakin nan da na ɗauka.

سأذهب لأبحث عما يخفف هذا الذنب الذي تحملته .

Ko da an gaya mini alhaki zai komo kaina.

مهما قيل لي أن الذنب سيعود عليَّ .

Alhakin waɗannan mutane da na yi rauni suna bisa wuyanta.

ذنب هؤلاء الناس الذين جرحتهم في رقبتها .

حِقَّةٌ ← Hikkatu أو Hik̃k̃a :

Hikakatu ita ce taguwar da za a iya aza mata kaya a bayanta , kuma namijin rak̃umi zai iya yi mata barbara.

الحقة هي الناقة التي يوضع على ظهرها الحمل ويطرقها الفحل .

Idan sun kai arba'in da shida za'a ba da hikkatu.

إذا بلغت ستة وأربعين يُعْطى حِقَّةٌ .

Idan yawansu ya kai casa'in da daya za'a ba da hik̃k̃a biyu.

إذا بلغ عددها واحدا وتسعين يُعْطي حقتان .

Za'a lissafta shi har ya kai hamsin sa'an nan a ba da hik̃k̃a daya.

يجب حتى إذا وصلت خمسين يُعْطِى حِقَّةً واحدة .

حقد ← Hik̃idu :

Wanda ya sa hik̃idu a zuciyarsa , ba zai ci gaba ba a rayuwarsa.

من جعل الحقد في قلبه لا يتقدم في حياته .

Kar ka yi wa dan'uwanka musulmi hik̃idu. لا تحقد على أخيك المسلم .

حقيقة ← Hakika :

تأتي بمعنى حقيقة أو إنَّ

Suna lura a cikin hakkin zatinsa. يتفكرون في حقيقة ذاته .

Mutanen na ganin sarki ya yi alheri , ba su san hakikanin dalilin kyautar ba. يرى الناس الأمير يفعل الخير ، ولا يعرفون حقيقة سبب الخير .

Ba a sani hakikanin wanda ya yi ba. لم تعرف حقيقة مافعل .

Na hak̃ik̃ance zaka share mini hawaye. تحققت أنك ستمسح لي دموعي .

Ta ga buta a yashe , sai ta dawo ta hak̃ik̃ance aljannu suka ɗauke shi.

رأت الإبريق مرميّا ، فعادت وتأكدت أن الجن أخذوه .

Hakika Allah ne ya ƙaddara shi. أنَّ الله قدره .
Hakika Allah ya san abin da ya halitta أن الله يعلم ما خلق .
Hakika ka koya babban abu. إنك عَلَّمْتَ أمرا عظيما .

حَـكم ← Hukunta :

Sarki ya ajiye ni nan , in hukunta dukan wanda ya yi laifi.
وضعني الأمير هنا لأحاكم كل من يخطيء.
Sabo da haka suka dangana bisa ga hukuncin Allah.
لذلك صبرنا على حكم الله .
Aka yi masa hukunci. حُكِم له .
Ya naɗa shi hakimi. عينه حاكما .
Gidan nan ba na wani hakimi ba ne. هذا البيت ليس بيت حاكم .
Sarkin gari ya fidda hakimai hudu daga sarauta.
أمير المدينة أخرج أربعة حكام من السلطة .
Zai kai maganar gaban hukuma. سيحمل الأمر إلى الحكومة .

حِكْمة ← Hikima :

Shi ba abin da ya fi so , sai hikima. لايحب شيئا اكثر من الحكمة .
Ubangiji ya ba shi hikima fiya da dukan sauran mutane.
وهبة الله الحكمة اكثر من كل الناس الآخرين .
Da suka ga ya fito , suka tare shi , suna yabonsa a kan wannan hikima. عندما رأوه خرج ، قابلوه ومدحوه على هذه الحكمة .
Rubuta wannan karin magana , cikin littafin da ke tsara hikimomi.
اكتب هذا المثل في الكتاب الذي يضم الحِكَمَ .
Yaro mai hikima irinka ban taba ganinsa ba.
وَلَد حكيم مثلك لم أره في حياتي .
Ya kamata mu gode wa masu hikimar da suka fito mana da waɗannan abubuwa. يجب أن نشكر الحكماء الذين خرجوا لنا بهذه الأشياء .

حكاية ← Hikaya :

Hikayoyin larabawa suna da yawa. حكايات العرب كثيرة .

In ka zauna da tsofaffi zaka san hikayoyin da.

إذا جلست مع الشيوخ ستمسع حكايات الماضي .

Na karanta wata hikaya mai ban dariya. قرأت حكاية مضحكة .

حِلٌّ ← Hillu :

Ya yanka a Marwa bayan da ya shigar da ita Hillu.

ذبح في المروة بعد أن ذحل بها من الحِلِّ .

Wanda ya nufi yin Umra ba zai yi harami na yinta ba , daga cikin Makka har sai ya fita Hillu.

من أراد العمرة من مكة ، ولم يحرم من خارجها خرج إلى الحِلِّ .

حَلَّ ← Halatta :

Bai halatta gare shi ba , ya jinkirta tuba. لايحل له أن يؤخر التوبة .

Bai halatta ga mai haila ba ta yi salla ko azumi.

لايحل للحائض الصلاة أو الصيام .

Bau halatta gare shi ba abutan fasiƙi ko zama da shi.

لايحل له صحبة الفاسق أو الجلوس معه .

حال ← Hali أو Alhali :

تأتي بمعنى طبع أو خلق

Ba ta bar halinta ba, لم تترك طبعها .

Mata duk halinsu ɗaya ne. النساء حالهن كله واحد .

Ta shiga ba shi labarin yadda halin wurin yake.

أخذت تقص عليه كيف حال المكان .

Na san halin maza sarai , shi ya sa ba na yarda.

عرفت حال الرجال تماما ، وهو الذي جعلني لا أوافق .

In na ga halin zama , me zai hana ne ?

إذا رأيت فرصة للبقاء ، فماذا يمنعني ؟

Rai ya yi hakinsa. الموت عمل حاله أي مات .

Babu laifi wajen ambaton halayensu. لا بأس من ذكر أحوالهم .

Akwai halaye bi da bi ga sallar farilla.

يوجد سبعة أحوال متتابعة لصلاة الفرضية .

Wace wautar zata ɗebe ni in riƙa ɓata lokacina alhali ko na san jama'a ba su kula da wahalar da nake sha ba ?

أي غباء يجعلني استمر في إضاعة وقتي بينما أعرف أن الناس لا يهتمون بالمشاكل التي أواجهها .

Wanda kuma ya fita bai yi sallar azahar da la'asar ba , alhalin rana ya rage gwargwadon yin raka'o'i uku sai ya sallace su a matsayin na tafiya.

من خرج ولم يصل الظهر أو العصر ــ بينما بقي من النهار قدر ثلاث ركعات صلاهما سفريّتين .

Idan ka fuskanci rana da fuskarta , alhajin kana tsaye , ba ka ɗaga kanka ba . Idan ka ga rana da idonka , lokaci ya yi.

إذ استقبلت الشمس بوجهك بينما أنت قائم ، ورأيت الشمس بعينك فقد دخل الوقت .

حلال — Halas أو Halal :

Kome ya same su halas ne. كل ما أصابهم حلال .

Kome aka yi wa dan halas sai ya rama. كل ما يُفعل لابن الحلال يرده .

Babban mugun abu ga ɗan halas , ya tasam ma munafunci.

أسوء أمر لابن الحلال أن يقصد النفاق .

Ya ƙi shiga mayaƙan , don ya san wannan yaƙi ba halal ba ne.

رفض الدخول مع المحاربين لأنه عرف ــ أن ــ هذه الحرب ليست حلالاً .

Ije dukan wanda ya nufi cutarka , halal ne ga shari'a.

دفع كل من يريد إيذاءك حلال في الشرع .

: Alewa — حلاوة

Alewa ta sake daskarewa. تجمدت الحلاوة مرة أخرى .

Ya aza kansa bisa alewa. وضع رأسة على الحلوى .

Wani ɗan alewa kuma ya ba da wata dabara. قدم شخص حلواني حيلة .

In ka ga yadda Fiti ke alewa da doki sai abin ya ba ka al'ajabi.

إذا رأيت كيف الفيتي يلعب بالحصان أخذك العجب .

: Himili — حِمْلٌ

Ya dauko himilin kaya. أخذ حملا من المتاع .

Wannan himilin kayan ina zaka kai sa ?

هذا الحمل من المتاع إلى أين ستحمله ؟

Ba zan iya wanke wannan himilin kaya ba.

لن استطيع غسل هذا الحمل من المتاع .

: Hamdala — حمد الله

Idan ya ɗaɗa da yin hamdala da hailala cikin kabbararsa ya kyauta.

إذا جمع مع التحميد والتهليل التكبير فهذا أحسن .

Ba ni da sauran bukata sai hamdala. ليس لي حاجة أخرى غير حمد الله .

Ya yi atishawa sau uku ya yi hamdala. عطس ثلاث مرات وحمد الله .

Bayan ya sha ruwa ya yi hamdala. بعد أن شرب الماء حمد الله .

: Hamada — حمادة

Mutum ba zai kama ɓataccen raƙumi daga hamada ba.

لا يأخذ الرجل ضالة الإبل من الصحراء .

Ba inda ake samun gishiri daga Ƙasarmu sai ta hamada.

لا يوجد مكان به الملح في بلدنا إلا الصحراء .

A cikin hamada akwai wata irin iska mai ban tsoro.

في الصحراء يوجد نوع من الرياح مخيف .

Ayari suka tsayawa su shirya su ɗebi ruwa kafin su shiga cikin babbar hamada. وقفت القافلة واستعدت لورود الماء قبل أن تدخل في الصحراء الكبرى .

حَوْلَ ← Haula :

Al'amarin ya kai la haula. بلغ الأمر غايته .

In masifa ta auku a gari sai lahaula wala Ƙuwwata.

إذا وقعت المصيبة في بلد فلا يردها إلا الله .

حيًّا ← Hayyan :

Yana nan hayyan. حي هنا .

Ko cikin hayyacinsa bai fi sule uku ba.

حتى في حياته لم يزد عن ثلاث شلنات .

حيران ← Hairani :

تأتي بمعنى خصومة أو مشاجرة

Musa sun yi hairani da matarsa. موسى في خصومة مع زوجته .

Wasan banza shi yake jawo hairani. اللعب المحرم هو الذي يجلب المشاجرة .

Kada ka yarda ka yi hairani da iyayenta.

لا ترضى أن تكون في خلاف مع والديك .

: Hila ← حيلة

Matar hila take yi masa don ta zambace shi.

فعلت المرأة له حيلة لتسخر منه .

Sannu sannu har hilolin nasa suka kama manyan gari.

رويدا رويدا حتى دخلت حِيَلَةُ على كبار المدينة .

: Haila ← حيض

Wanka na wajaba da sababin uku janaba da haila da jinin biƙi.

الغسل واجب بسبب أمور ثلاثة الجنابة ، والحيض ودم النفاس .

Bai halatta ga mai haila ba ta yi salla. لا يحل للحائض الصلاة .

★★★

الخاء

: **Ha'ini** ← خائن

Na tabbata Umaru ba ha'ini ba ne. تأكدت أن عمر ليس خائنا .
Kar ka sa ha'ini a kan dukiyarka. لا تضع الخائن على أموالك .
Wanda ya yi maka ha'inci kowani ya faɗi gaskiyarsa , ba zaka yarda ba. من خانك ، إذا قال لك كل واحد أنه صادق ، لا تصدقه .
Idan ya ji gargaɗin , sai ki gani ya daina ha'inci.
إذا سمع التحذير ، ترين أنه ترك الخيانه .

: **Habarta** ← خبر

تستعمل بمعنى قال

Ya habarta wa sarki ƙofa dukan abin da ya same shi.
قال لحارس البوابة كل ما حدث له .
Ya tambaye ta labari , duk ta habarta masa tun daga farko har zuwa ƙarshe. سألها عن القصة ، فقالت له كل شيء من الأول إلى الأخر .
Da zuwansa sai suka habarta masa duka abin da ya auku.
عند حضوره قالوا له كل ما حدث .

: **Hatimi** ← خاتم

Ya ga rubutan sarki ga kuma hatiminsa. رأي كتابة الأمير وها أيضا خاتمه .

Ya ɗauki hatimin sarki , zai kai majalisa ya ajiya.

أخذ خاتم الأمير ، سيذهب إلى مجلسه ليضعه .

Aka sanya mata hatimin shaida. وضع لها الخاتم كشاهد .

Ya buga hatiminsa ya kai mata. وضع خاتمة وحملة لها .

: Hidima ← خدمة

تأتي بمعنى عمل أو وظيفة أو مهمة

Ya yi masa ko wane irin hidima tasa. أدي له كل خدمته .

Har wa yau kuwa zuriya bayin nan suke yin wannan hidima.

حتى إلى اليوم ذرية هذا الخادم يقومون بهذه الخدمة .

Yayin da kowa yana cikin hidimarsa sai muka ji kuwwa daga waje.

بينما كل في عمله سمعنا صراخا من الخارج .

Aka kai Tanko kurkuku , aka shiga hidimar naɗin sarauta.

حمل تنكو إلى السجن وبديء في مهمة تولية السلطة .

Sauran iyalin kuma suna can suna ta hidimarsa. باقي الأسرة هناك يخدمونه .

: Haraba ← خرابة

ساحة واسعة تترك أمام المسجد للمصلين

Akwai haraba mai faɗi ana shiga ta ƙofofi hudu.

توجد ساحة كبيرة يدخل إليها من أربعة أبواب .

In jumma'a ta yi , an cika masallacin kan dauka 400 ko fi ban da haraba da sararin waje.

إذا جاءت صلاة الجمعة ، ملئت المصلى التي تأخذ ٤٠٠ أو يزيد ، عدا الساحة والفضاء الخارجي .

خراج ← **Haraji** :

Ya tafi ƙasar sarkin arewa don ya taimake shi karɓar haraji.

ذهب بلدة أمير الشمال ليساعدة في جمع الخراج .

Batun haraji da na yi maka jiya , ba ka ce kome ba.

مشكلة الخراج التي عرضتها أمس ، لم تقل شيئا عنها .

Yanzu zaune yake kawai , ba ya biyan haraji.

الآن يجلس فقط ، لا يدفع الخراج .

خزف ← **Hazafi** :

Girman tsakuwar ana so ta zama kamar tsakuwar hazafi.

حجم الحصي المراد يفضل أن يكون مثل حصي الخزف .

خسارة ← **Hasara** أو **Asara** :

Bakinku ya jawo muku hasara ke nan. فمكم جلب لكم الخسارة .

Ya kamata in ba shi kuɗinsa don kada in mutu in yi masa hasara.

يجب أن أعطية ماله لكيلا أموت وأسبب له الخسارة .

Faduwar gaba hasarar namiji. الجبن عيب الرجل .

Ba na dai yarda in yi asara a wofi. لا أوافق أن أخسر عبثا .

Haka kuke sha shayenku kana sa mutane asara wofi.

هكذا تشربون شريكم وتخسّرون الناس عبثا .

خسوف ← **Husufi** :

Sallar husufi sunna ce wajiba. صلاة الخسوف سنة واجبة .

Ba a yin jam'i ga sallar husufin wata. ليس في صلاة خسوف القمر جماعة .

Babu huɗuba rubutacciya a ƙarshen sallar husufin rana.

ليس في آخر صلاة خسوف الشمس خطبة مكتوبة .

خط ← Haɗɗi :

تعنى ضرب الرمل أو التنجيم

Na share ƙasa sai ka ce mai shirin haɗɗi na zana wata alama.

كنست الأرض كمن يستعد لضرب الرمل ورسمت علامة .

Ko da yake ni ban iya haɗɗi ba , wannan ƙarya ce.

مع أنني لا أعرف التنجيم ، هذا كذب .

خطأ ← Haɗa'i :

Yin abin da bai kamata ba a gaban yara haɗa'i ne.

فِعْل مالا ينبغي أمام الأولاد خطأ .

Babban haɗa'i ne zagin 'ya'ya wani.

اكبر خطأ أن تسب أبناء غيرك .

خطبة ← Huɗuba :

Yin huɗuba a cikin sallar jummu'a wajibi ne.

الخطبة في صلاة الجمعة واجب .

Babu huɗuba rubutacciya a ƙarshen sallar husufin rana.

ليس في آخر صلاة خسوف الشمس خطبة مكتوبة .

Ya miƙe yana dogara a kan sanda sai ya yi huɗuba.

قام معتمدا على العصا وخطب .

خطر ← Hatsari أو Haɗari :

Tsayawa a wuri mai haɗari wajen tsoron gari yana da falala mai yawa.

للوقوف في المكان الخطير ــ الرباط ــ عند الفزع فضل عظيم .

Ya gaya masa dukan haɗari da ya same shi.

قص له كل الخطر الذي واجهه .

Hadarin da ka shiga sau biyu ba su ishe ka ba ?

الخطر الذي دخلت فيه مرتين لم يكفك ؟

Ga hatsari game da namun daji da macizai.

ها الخطر والحيوانات المفترسة والثعابين .

Ubangiji mai iya kuɓutar da duk bayinsa ne daga dukan hadura.

الله القادر على تخليص عبادة من كل الأخطار .

: Husuma ← خصومة

Shaidar abokin husuma ko tuhuntacce ba ta halatta.

شهادة الخصم أو المتهم لا تجوز .

Wannan dan duniya , ya zo , ya gama mu da husuma.

هذا الشقي ـ الدنيوي ـ جاء وسبب لنا الخصومة .

Ba yawon da nake yi , sai na yi da mutane da gama husuma.

لا اتجول في مكان إلا وأجعل الناس يقعون في خصومة.

: Huffi ← خُفٌّ

Ya yi shafa a kan huffi. مسح على الخف .

Ya sanya hannunsa na dama a kan huffi. وضع يده اليمني على الخف .

Mace zata sanya huffi da tufafi a cikin haraminta.

المرأة تلبس الخف والثياب في إحرامها .

Namiji ba zai sanya huffi ba a cikin haraminsa.

الرجل لا يلبس خفًا في إحرامه .

: Khul'i ← خُلْعٌ

Khul'i shi ne sakin zare jiki wanda mace ke yi zuwa ga mijinta ta hanyar miƙa masa abu muhimmi.

الخلع هو طلقة لا رجعة فيها حيث تعطي الزوجة للزرج شيئا مهما يخلعها به من نفسه

: Hilafa ← خلاف

Hilafa tsakanin ba malamai sabon abu ba ne.

الخلاف بين العلماء ليس أمرا جديدا .

Akwai hilafa tsakanin mazhabobi. يوجد خلاف بين المذاهب .

An sami wata 'yar hilafa tsakanin ɗa da ubansa.

وجد خلاف بسيط بين الأبن وأبيه .

: Halifa ← خليفة

Allah ya saukad da Adamu halifarsa daga cikin aljanna tasa.

أنزل الله آدم خليفته من جنته .

Halifa ya umurce fadawarsa da dukan mutanensa da iyalinsa , su mai da Hasan kamar shi ne halifa.

أمر الخليفة حاشيته وكل أهله ورجاله أن يجعلوا حسن كأنه الخليفة .

: Halitta ← خلق

Allah ya halicci wuta ya tande ta gidan azaba ne ga wanda ya kafirci.

خلق الله النار وأعدها دار عذاب لمن كفر .

Manyan azalumai biyu ne Allah ya halitta a duniya daga ubanka da kura. أكبر الظالمين أثنان خلقهما الله في هذه الدنيا ، أبوك والذئب .

Mahaliccin baƙi da fari shi ne Allah. خالق الأسود والأبيض هو الله .

Halittaan sama da ƙasa duk bayi ne na Allah.

مخلوقات السماء والأرض كلها عبيد الله .

Alƙur'ani bai zamo halittacce ba balle ya halaka.

القرآن ليس مخلوقا فيفني .

: Alhamis ← خميس

Da Fasih ya ga alhamis ne , sai ya ƙi zuwa wajen malaminsa.

عند ما رأي فصيح أن اليوم الخميس ، رفض الذهاب إلى معلمه .

Ba a ko karatu alhamis.

لا تكون دراسة يوم الخميس .

Zan gamu da shi ranar alhamis mai zuwa.

سألتقي معه يوم الخميس القادم .

: Humusi ← خُمْسٌ

Mun samu sisi mu biyar , sabo da baka , kowa ya samu sisi ke nan.

وجدنا قرشا نحن الخمسة ، لذلك نال كل واحد خُمْسَ قرش .

Rabona ne a cikin wannan gado humusi ne.

نصيبي في هذا الميراث الخُمس .

An karɓar humusin rikiza.

أُخِذَ خُمْسُ ركاز .

: Hamsin ← خمسين

Za'a lissafta shi har ya kai hamsin sa'an nan a ba da biƙƙa ɗaya.

سيُحسب حتى إذا بلغت خمسين يُعْطي حقَّةٌ واحدةٌ .

Kafin kwana hamsin cikin fam goman nan saura duka bai fi sule sittin.

قبل خمسين يوما هذه العشرة جنيهات لم يبق منها أكثر من ستين شلنا .

Sarki ya sa aka tara masa manyan malamai guda hamsin na ƙasarsa.

أمر الأمير أن يُجْمَع له خمسون من كبار علماء بلده .

: Alhanziri ← خنزير

Allah ya haramta cin mushe da jini da naman alhanziri.

حرم الله أكل الميتة والدم ولحم الخنزير .

Ba mai cin alhanziri sai arna. لا يأكل الخنزير إلا الوثني .

Alhanziri da muni yake. الخنزير سيء .

خَوَلٌ ← Kawali :

تأتي بمعنى قواد النساء

Kawali da mai zina duk wuta zasu shiga in ba su tuba.

القواد والزاني سيدخلان النار إن لم يتوبا .

Kawali mai kwadayin kwaɓo ran gamonsa da Allah ya kaɗe.

القواد الذي يشتهي القرش يهلك يوم لقائه بالله .

Ba mai yin kwalanci sai watsatse. لا يحترف القوادة إلا فاسد .

خير ← Alheri أو Hairan :

Wanda ya aikata aikin alheri ko da misalin ƙwayar zarra ce zai gan shi. من عمل مثقال ذرة خيرا يره .

Ka ba da gaskiya da ƙadara alherinsa da sharrinsa.

تؤمن بالقدر خيره وشره .

Aikata alheri wa kowa sakayyarka tana wurin Allah.

افعل الخير مع الجميع وثوابك عند الله .

Allah ya saka maka da alheri. جزاك الله خيرا .

Sau da yawa mutum ya kan ƙi abu ya zo ya zama hairan gare shi.

مرات كثيرة يكره الإنسان شيئا فيأتي ويكون خيرا له .

In ka aikata hairan zaka ga hairan. إن فعلت خيرا سترى خيرا .

★★★

الدال

: **Da'ira** ← دائرة

Wannan shi ma a cikin da'ira ake yin shi. هذه اللعبة أيضا تُلْعب في دائرة .
Yara sun yi da'ira a filin makaranta. عمل الأولاد دائرة في فناء المدرسة .
Daga cikin tasoshin nan waɗansu da'irori. من هذه الطاسات البعض دوائر .

: **Da'iman** أو **Da'ima** ← دائم

Ya yi mana sutura da'ima. سترنا سترة دائمة .
Da'iman ba na iya barci sai na ƙoshi. دائما لا استطيع أن أنام إلا إذا شبعت .
Na fahimci ba wanda yake sace mini nama da'iman sai mage.
فهمت أنه لا يسرق مني اللحم دائما إلا القطة .

: **Dabba** ← دابَّة

تأتي بمعنى حيوان

Jemage ya ce shi ba dabba ba ne. قال الخفاش أنه ليس حيواناً .
Sarkin dabbobi ya aika wurin jemage ya ce shi ba dabba ba ne.
ملك الحيوانات بعث إلى الخفاش وقال أنه ليس حيوانا .
Zaki shi ne sarkin dabbobi. الأسد هو ملك الحيوانات .
Zakkar dabbobi farilla ce. زكاة الماشية فريضة

: **Dubura** ← دُبُر

Ya goge duk abin da yake na ƙazanta daga dubura.

مسح كل ما يوجد من قذارة في دبره .

Basur ya zage wa Lada dubura. الباسور أحاط بدبر لادو .

Kar ka sadu da matarka ta dubura. لاتنكح امرأتك في دبرها .

: **Dabara** ← دبَّر

تأتي بمعني حيلة

Ina dabara ? ما الحيلة ؟

Ta yi dabara , ta kwanta rigingine ta buɗe baki kamar ta mutu.

عملت حيلة ، رقدت على ظهرها وفتحت فمها كأنها ماتت .

In kin ji shawarata kada ki nuna masa kin gane dabararsa.

إذا سمعتي مشورتي لا تظهري له أنك فهمتي حيلته .

Kullum darasi ya fado a kan dabarun da ya kamata su yi.

دائما الدرس يكون على الحيل التي يجب أن يعملوها .

: **Dujal** أو **Dijal** ← دَجَّال

Ina neman tsari da kai daga jawabin masifar Dijal.

أعوذ بك من مصيبة الدجال .

Dijal idonsa ɗaya ne a goshi. الدجال له عين واحدة في جبهته .

Dujal zai bayyana a ƙarshen duniya. الدجال سيظهر في نهاية العالم .

: **Darassalamu** ← دار السلام

Allah ya sake tara mu a Darassalamu.

اللهم أجمعنا مرة أخرى في دار السلام .

Allah ya ƙaddara saduwarmu a Darassalamu.

قدر الله أن يجمعنا في دار السلام .

: Daraji ← درجة

Allah ya ɗaukaka darajarsu a cikin aljanna. رفع الله درجتهم في الجنة .

Bayi zasu ƙetare shi da gwargwadon darajar ayyukansu.

العباد يجتازونه بقدر درجة أعمالهم .

Kada a faɗi darajar sai kuwa ya ƙare bayyana.

لا تقل الدرجة حتى ينتهي الكل من الشرح .

Mutum ya kamata ya kula da abinci mai daraja a jikinsa.

يجب على الانسان أن يهتم بالطعام المفيد لجسمه .

Daga nan daraja sarkin fada ta ragu wajen sarki.

من هنا نقصت منزلة رئيس القصر لدي الأمير .

Ina roƙo a cikin darajar mulkinka ka bar ni in yi 'yan kwanaki, kaɗan a nan. أسألك بعظمة ملكك أن تتركني أمكث أياما قليلة هنا .

Ya karya mini daraja. أنقص قيمتي .

Ya duba kayan ɗaki , ta ga duk an kwashe masu daraja.

نظرت إلى أثاث الحجرة ، فرأت أن كل ما أخذوه قيّم .

: Darasi ← درس

Jatau ya koyi darasi. جاتو تَعَلَّم درساً .

Kullum darasi ya faɗo a kan dabarun da ya kamata su yi.

دائما الدرس يكون على الحيل التي يجب أن يفعلوها .

Musa ya karanta darasi mai wahala. موسى قرأ درسا صعباً .

A ranar alhamis babu darasi a makarantu.

في يوم الخميس لا توجد دراسة في المدرس .

Kullum Isa ba ya makara a wajen darasi.

دائما عيسى لا يتأخر عن الدرس .

: **Dir'i** ← درع

Abin da ake ce wa dir'i shi ne riga. — القميص هو ما يُقال له الدرع .

: **Dirhami** ← درهم

Ba yin zakka ga azurfa da yawanta bai kai dirhami dari ba.
لا يُزَكي عن الفضة التي لم تبلغ مائة درهم .
Dirhami ɗari kuwa shi ne aukiya biyar. — المائة درهم تساوي خمس أوقيات .
Ba ni ke dirhami. — ليس عندي ولا درهم .

: **Durwa** ← دروة

تأتي بمعني سترة

Mace ba ta durwa sai da dalili. — لاتضع المرأة السترة إلا لسبب .
Amfanin da auduga ya hana mata yin durwa da tsumma.
فائدة القطن جعلت النساء لايتحفظن بالخرقة .
Musa ya yi durwa a bakin kogi. — موسى عمل دروة على شاطيء النهر .

: **Addu'a** ← دعاء

Zaka yi addu'a cikin sujjada in ka ga dama.
ادع في سجودك إن وجدت الفرصة .
Da ya yi sallama ya yi addu'a. — عندما سلَّم دعا .
Aka yi mana addu'a don kada shaidan ya sake wasa da zukatammu.
دُعِيَ لنا لكيلا يلعب الشيطان مرة أخرى بقلوبنا .
Ya yi masa kyakkyawar addu'a. — دعا له دعاءً حسناً .

: Da'awa ← دعوى

Mun ji da'awa tasa yanzu mu ji taka. سمعنا دعواة الآن نسمع دعواك .

Wanda ake da da'awa a kansa ya ƙi rantsuwa.

من ادُّعِيَ عليه رفض القسم .

